# RAHOTON AYYUKAN MAZAƁUN TARAYYA A JIHAR ZAMFARA

# NA

# 2020



*Da Tallafin:* MacArthur Foundation

# GABATARWA


Bin diddiƙin ayyukan raya-ƙasa a mazaɓun da ke Jihar Zamfara na daga cikin ayyukan Cibiyar Bincike da Ciyar da Arewa Gaba, wato "Arewa Research and Development Project" (ARDP) wadda Gidauniyar MacArthur ke tallafa wa a ƙarƙashin tsarin shirin tallafi na "On Nigeria 2.0". Ginshiƙin shirin na mayar da hankali ne kan ƙoƙarin hana ƙaruwar cin-hanci da rashawa ta fuskar taimakama shirye-shiryen ƙungiyoyin al'umma na tabbatar da aƙidojin tsare gaskiya da sa hannun al'umma cikin tsarin gudanar da mulki. Babban gurin wannan tsarin aiki shine ya auna ƙarfin sa hannun mutane wajen tantancewa da gudanar da ayyukan raya mazaɓu da kuma yin la'akari da sahihan bukatun al'ummar mazaɓun. Ana kautata zaton cewa wannan tsarin aikin zai kafa matakai ko kuma ya ƙara haɓaka hanyoyin da 'yan ƙasa zasu shiga cikin tsare-tsaren zaɓen ayyukan da kuma sa ido wajen aiwatar da su. Wannan tsarin aikin dai Kungiyar ARDP tare da haɗin guiwar Kungiyar ZamTracka ke jagorantarsa.

Kungiyar ARDP dai wata cibiya ce mai bincike da bata da alaƙa da gwamnati ko la'akari da wata siyasa, ƙabila, ko nuna bambancin addini wadda ayyukanta sun mayar da hankali wajen nazari da tantance manyan matsaloli da ke addabar Arewacin Nijeriya da al'ummarta, da yunƙurin samar da hanyoyin bincike da tsare-tsaren ayyukan da zasu magance matsalolin dake addabar yankin. Gurin Cibiyar shine ƙoƙarin samar da tafarkin bunƙasar tattalin arziki da kyautata rayuwar al'ummar yankin ta hanyoyin da zasu samar da haɗin guiwa tsakanin jama'a da hukomomin gwamnati wajen hada ƙarfi-da-ƙarfe  domin ciyar da al'umma gaba.

Ita kuwa ZamTracka, ƙungiya ce mai zaman kan ta da ke Gusau a jihar Zamfar, wadda ta ke yekuwar ganin ana yin taka tsan-tsan da dukiyar jama'a a cikin mulkin jihar. Fitattun ayyukan ta sune samowa da tantance bayanai kan tanade-tanaden ayyuka da ke cikin kasafin kuɗi na jihar Zamfara da kuma ayyukan raya-ƙasa a yankunan mazaɓu, da kuma yin amfani da su wajen wayar da kan al'umma. Manufa dai ita ce a taimaka wa jama'a wajen bin diddiƙin tanade-tanade kasafin kuɗi da yadda ake gudanar da ayyukan raya-ƙasa a mazaɓu. Ana sa ran cewa wannan yunƙuri zai sa a samu masu himma da dagewa wajen ganin ana gudanar da ayyukan raya-ƙasa na gwamnati da hukumominta tare da haɓaka yadda jama'a za su nemi samun ɗorarriyar hanyar tsoma bakinsu a cikin gudanar da al'amuran jiharsu.

# YAWAN AYYUKA

## A MAZAƁU




### Mazaɓun 'Yan Majalisar Dokoki

| | |
|---|---|
| Gusau/Tsafe | 3 |
| Kaura B/Magaji | 4 |
| Anka Mafara | 3 |
| Gummi/Bukkuyum | 3 |
| Bakura/Maradun | 3 |
| Shinkafi/Zurmi | 5 |
| Maru/Bungudu | 3 |

### Mazaɓun 'Yan Majalisar Dattijawa

| | |
|---|---|
| Zamfara ta Tsakiya | 3 |
| Zamfara ta Arewa | 10 |
| Zamfara ta Yamma | 4 |

# Karin Haske

Ayyukan raya-ƙasa na mazaɓu wasu ayyuka ne da wakilai a majalisun dokoki na tarayya ke ƙirƙirowa domin kawo ribar mulkin demokaraɗiyya ga al'ummominsu don haɓakar ci-gaban yankunan karkara. A kan gabatar da bukatun gudanar da waɗannan ayyukan ne ga sashen mulki a lokacin da ake tsare-tsaren kasafin kuɗi. Tsarin mulkin ƙasa ya tanadi cewa majalisun tarayya ke da alhakin sanya ido akan ayyukan gwamnati. Kasancewar 'yan majalisu ne ke ƙirƙirar ayyukan, ashe su ke da nauyin su riƙa yiwa jama'a bayanai akai-akai akan ayyukan. Wannan ya isa hujja saboda talakawa ba za su iya tunkarar hukumomin gwamnati cikin sauƙi ba kamar yadda za su iya tuntuɓar wakilan su. Domin ganin munbi diddiƙin waɗannan ayyukan raya ƙasa akan kari, mun yi amfani da jami'an mu waɗanda suka san wuraren da ake gudanar da takamaiman ayyukan.

A shekarar 2020 an ware jimillar kuɗi N2.389bn domin gudanar da ayyukan mazabu a jihar Zamfara, mafi yawansu ayyukan tallafi da wayar da kan jama'a ne ba manyan ayyuka da za a iya gano su cikin sauƙi ba.

Ya bayyana cewa ba a gudanar da aikin tantance buƙatu ba tare da ɓangarorin da za su amfana tunda ya kamata ne ayyukan an yi su ne don magance matsalolin jama'a. Yawancin ayyukan na tallafi ba su da ƙayyadaddun yanayi na tantance su a zahiri. Bugu da ƙari, tasirin irin waɗannan ayyukan wajen kyautata zamantakewar al'umma na da rauni.

Yawancin ayyuka ba su da mahimmanci wajen magance matsalolin zamantakewa. Misali, tsawon shekaru ana ta gabatar da ayyuka akan fina-finai a cikin jerin ayyukan raya ƙasa na jihar Zamfara. Ba a san jihar a matsayin cibiyar shirya fina-finai ko rarrabawa ba da zai cancanci irin wannan aikin na tsawon wannan lokaci. Irin waɗannan ayyukan a fili yake ba su da wani tasiri ga matsalolin jama'a.

A ƙarshe, yana da kyau a lura cewa mun ƙaddamar da shirn samar da matsayi ga 'yan majalisa akan ma'auni uku da zai tantance ƙoƙarinsu wajen gabatarwa da aiwatar da ayyukan raya ƙasa na mazaɓu. Addu'armu ita ce yin hakan zai samar da kyakykyawan fuskar diba ƙoƙarin su kuma ya taimaka wajen yin muhawara tsakanin jama'a domin taimakawa wajen ƙarfafa tafarkin gaskiya da rikon amana, kuma yayin da hakan zai iya kawo gasa mai ma'ana a tsakanin 'yan majalisa.

# SAKAMAKON AYYUKAN MAZAƁU NA SHEKARAR 2020 A TAƘAICE

▼

| 33 | 7 | 2 |
| --- | --- | --- |
| AN AIWATAR | BA A YI BA | ANA BISA YI |

# 42

JIMILLAR YAWAN AYYUKA

## JIMILLAR YAWAN AYYUKA

# 42

## JIMILLAR KUƊIN AYYUKA

# 2.389b

## Yawan Manyan Ayyuka

# 40%

A Cikin Jimillar Kuɗi

## YAWAN AYYUKA AKAN YANAYINSU

N1.247 Biliyan — Ayyuka 25

Ayyukan Tallafi da Bada Horo

N1.142 Biliyan — Ayyuka 17

Manyan Ayyuka

# 01

Yawan Ayyukan da aka
# GABATAR
4



## Sakamako

Sen. Muhammad Hassan Nasiha

Zamfara Ta Tsakiya

3
An Aiwatar

1
Ana kan yi

# Horo Akan Dabarun Kasuwanci da Sana'o'i ga Matasa

**Kuɗin Aiki: N44.285M** **Matsayin Aiki: An Aiwatar**

An aiwatar da wannan aikin sosai. Kimanin matasa 350 ne da suka fito daga sassa na wannan yankin majalisar dattawa (Gusau, Maru, Tsafe da Bungudu) aka zaɓo kuma aka raba su zuwa sassa bakwai (7) na kasuwanci daban-daban, wato:

1. Sarrafa Kwanfuta
2. Ɗinkin Hannu (Mata)
3. Ɗinkin Keke
4. Kitso (Mata)
5. Aski na Zamani (Maza)
6. Gyaran Wayar Salula
7. Aikin Kawata Mahalli

Shirin horon ya kasance na wata guda tare da tsauraran dokoki da hukunci don hana rashin zuwa. Wuraren bayar da horon sun watsu a sassan yankin majalisar dattawa kuma tawagarmu ta zagaya wasu wuraren da aka zaɓa domin ganin yadda aka gudanar da horon. Mun fahimci shirye-shiryen horarwa na da amfani sosai yayin da akwai kayan horo ga waɗanda aka horar don gwada fahimtarsu akan kasuwancin da suka zaɓa.

Bayan shirin horaswa, an baiwa kowane ɗaya daga cikin waɗanda aka horas tallafin kayan aiki na nau'in kasuwancin da ya sami horo akai.











# Samar da horo kan tsaftar muhalli da tsaftace kayan aiki ga matasa a Zamfara ta Tsakiya






**KuɗIn Aiki: N40m** **Matsayin Aiki: An Aiwatar**

Hukumar Kula da Lafiyar Muhalli ta Najeriya ce ta gudanar da wannan aiki a babban dakin taro na Sakatariyar Jibril Bala Yakubu. Kimanin masu aikin sa kai 1000 ne aka horar da su kan ƙananan sana'o'in abinci irin su Kuli-Kuli, dafaffen ganyen zogale, Akara, da kuma kiwon kaji da yankan farce. An ba da horo na musamman kan yadda ake tsabtace kayayyakin sana'a don ingantacciyar lafiya da tsafta ga masu sayarwa da masu saye.



A ƙarshen horon, Hukumar ta ba wa mahalarta takardar shaidar horon, kuma an ba kowannensu tallafin Naira Dubu Goma (N10,000). Taron ya samu halartar manyan baƙi da suka hada da mataimakin gwamnan jihar Zamfara da shugabannin ƙananan hukumomi da sauran jami'an gwamnati.

# Bunƙasa wurin yawon buɗe ido a Kwatarkwashi a Zamfara ta Tsakiya

**Kuɗin Aiki: N50m** **Matsayin Aiki: An aiwatar**

Aikin babba ne, saboda ya ƙunshi abin da za a yi amfani da shi tsawon shekaru. Sanatan mazaɓar ne tare da ɗimbin jama'a suka halarci bikin ƙaddamar da aikin a ƙauyen Kura da ke kusa da garin Kwatarkwashi a Karamar Hukumar Bungudu.

Masu tantance aikin sun fara bin diddiƙin aiwatar da shi a watan Satumba na 2020 kuma sun shaida cewa an gudanar da ayyukan gine-gine masu yawa. Tawagar ta sake kai ziyara bayan an kammala domin tantance girman aikin. Wurin dai na masu ziyara yawon buɗe ido ne wanda aka ƙawata da abubuwan ban sha'awa da suka haɗa da zane-zane akan dutse, da filin wasa na yara.

Wannan aiki an tsara shi ne don samar da kuɗaɗen shiga ta hanyar yawon shaƙatawa, wanda idan aka sarrafa shi tare da kula kamar yadda ya kamata, zai iya ba da gudummawa ga bunƙasar tattalin arzikin al'ummar wannan karkara.


















# Shirin samar da rijiyoyin burtsatse masu amfani da hasken rana a Zamfara ta Tsakiya

Kudin Aiki: N130m

Matsayin Aiki: An Aiwatar

Aikin rijiyar burtsatse mai amfani da hasken rana an yi shi ne domin magance matsalar ƙarancin ruwan sha da ake fama da shi a wasu yankunan dake faɗin mazabar. An raba tsarin rijiyoyin burtsatse zuwa kashi biyu: Rijiyoyin burtsatse masu amfani da hasken rana da rijiyoyin burtsatse na tuƙa-tuƙa.

A tsarin rabon, Karamar Hukumar Gusau tana da rijiyoyi guda 11, Karamar Hukumar Tsafe tana da guda 9, Karamar Hukumar Bungudu tana da guda 5, Karamar Hukumar Maru na da guda 3. Sai dai Karamar Hukumar Gusau ce kawai ke da rijiyoyin burtsatse 6 masu amfani da hasken rana. Gaba ɗaya an haƙa rijiyoyin burtsatse guda 34 ne a mazabar.


















02

Yawan Ayyukan da aka

# GABATAR

3

# Sakamako

3

An Aiwatar

0

Saura



Hon. Kabiru Ahmadu Mai Palace

Mazaɓar

Gusau/Tsafe

# Samar da Keke Napep a Mazaɓar Tarayya ta Gusau/Tsafe

Kuɗin Aiki: N50m

Matsayin Aiki: An Aiwatar

An gudanar da wannan aikin ne a ranar 7 ga Nuwamba, 2020 a wani biki da aka gudanar a Gidan Dutsi da ke Gusau. An sayo sabbin Keke Napep guda 65 kuma an raba su ga zaɓaɓɓun mutane a wannan mazaɓar.

Mun gano cewa galibin waɗanda suka ci gajiyar wannan tallafi magoya bayan ɗan majalisar ne saboda ba a gudanar da wani tsarin tantance waɗanda suka fi dacewa da irin wannan tallafi ba. Wannan ya kasance al'adar tsarin kusan dukkanin ayyukan tallafi a duk faɗin Jihar.

















# Samar da Babura a Mazaɓar Tarayya ta Gusau/Tsafe

Kuɗin Aiki: N31m

Matsayin Aiki: An Aiwatar

An gudanar da wannan shirin ne a garin Tsafe a rana ɗaya da shirin rabon kekunan Napep na Gusau. Ko da yake wasu gungun mutane ne dabam suka ci gajiyar wannan rabon, har yanzu mun lura da son zuciya iri ɗaya ta fuskar zaɓen masu cin gajiyar. 'Yan kore da magoya bayan siyasar ɗan majalisar sun kasance mafi yawan wadanda suka ci gajiyar wannan shirin bada tallafi.

A jimlace, an rarraba babura 190 na nau'i/samfuri daban-daban.

















# Horar da Matasa a Gusau da Tsafe

**Kuɗin Aiki: N40m**

**Matsayin Aiki: An Aiwatar**

Hukumar Raya Al'ummomin Kan Iyaka ce ta aiwatar da wannan aikin a watan Yuli na shekarar 2020. An zaɓo mutane 350 da suka amfana a mazabar kuma an horar da su a kan sana'ar ɗinki na tsawon kwanaki 2. Duk waɗanda suka ci gajiyar tallafin mata ne da aka horas da su kan sana'ar dinki don dogaro da kansu.

A ƙarshen horon, an raba injunan ɗinki na hannu ga duk waɗanda aka horas.

















# 03

## Yawan Ayyukan da aka Gabatar

# 3



**Sulaiman Abubakar Mahmud Gummi**

Mazaɓar

Gummi/Bukkuyum

## Sakamako

3

An Aiwatar

0

Saura

# Shirin Horas da Matasa akan dogaro da kai da zaman lafiya a Gummi/Bukkuyum

**Kuɗin Aiki: N41m** **Matsayin Aiki: An Aiwatar**

Matasa 400 ne a mazabar, 200 daga Gummi da 200 daga Bukkuyum, aka zaɓo domin gudanar da wannan shiri. Sun ƙunshi duka jinsi biyu kuma kaɗan daga cikin waɗanda suka amfana sun kasance masu raunin lafiyar jiki ne. Waɗanda suka ci gajiyar shirin sun sami jerin laccoci kan mahimmancin dogaro da kai, da dabarun magance rikice-rikice da samun yanayin zaman lafiya a cikin al'umma.


A ƙarshen shirin horaswar, kowanne daga cikin waɗanda suka ci gajiyar shirin ya samu tallafin kuɗi Naira 10,000, riga da hula masu tambarin shirin, da wasu kayan abinci. An gudanar da horon na kwana ɗaya a kowace ƙaramar hukumar ta Gummi da Bukkuyum.















# Samar da kujeri da teburan karatu a mazaɓar Gummi/Bukkuyum

Kuɗin Aiki: N40m	Matsayin Aiki: An Aiwatar

Waɗanda suka ci gajiyar wannan aikin sun kasance makarantun sakandare guda huɗu (4) a Gummi da Bukkuyum. Gabaɗaya, an ba da kujerun ajujuwa 350, da kujerun ofis na ma'aikata 150, da allunan rubutu na zamani 100 ga:

1. Makarantar Sakandare ta Jeka-ka-Dawo, Bukkuyum.
2. Makarantar Sakandare ta Mata, Bukkuyum.
3. Makarantar Sakandare ta Jeka-ka-Dawo, Gummi.
4. Makarantar Sakandare ta Mata, Gummi.





# Gyaran mayankar dabbobi a Gummi/Bukkuyum

Kuɗin Aiki: N40m	Matsayin Aiki: An Aiwatar

Tawagarmu da ta bi diddiƙin wannan aiki ta gano cewa an aiwatar da shi yadda ya kamata. A haƙiƙa, aikin ba gyaran mayankar dabbobin da ake da su ba ne, amma, ya kasance an gina sabbin ne a duka garuruwan Gummi da Bukkuyum.



04

Yawan Ayyukan da aka

# Gabatar

3



**Hon. Kabiru Yahaya (Classique)**

Mazaɓar

Anka/Mafara

# Sakamako

3

An Aiwatar

0

Saura

# Horo da Tallafawa Matasa a Mazaɓar Anka/Mafara

**Kuɗin Aiki: N60m** **Matsayin aiki: An Aiwatar**

A kan wannan aikin, an zaɓo jimillar mutane 150 da suka ci gajiyar shirin, waɗanda suka kunshi maza 90 da mata 60. An horar da su a kan sana'o'i iri biyu: rini (Maza) da yin taliya (Mata). An gudanar da horon na tsawon kwanaki 5, kuma a ƙarshen shirin kowane ɗaya daga cikin waɗanda suka ci gajiyar shirin ya karɓi Naira 50,000. Hakazalika, an kuma raba kayayyakin aiki ga duk waɗanda suka ci gajiyar tallafin. An bai wa mazaje dutsen guga, launuka, yadi na tufafi, bokiti, duro, da sitaci. An ba wa mata buhun fulawa mai nauyin kilogiram 50, da jarka ta mangyada mai lita 25, injin yin taliya, da kwano.










# Horaswa kan ayyukan haƙar ma'adinai a mazaɓar Anka/Mafara

**Kuɗin Aiki: N31m**

**Matsayin Aiki: An Aiwatar**

An aiwatar da wannan shirin a wajen Jiha. Shirin horon ya gudana ne a Jos, kuma an aiwatar da shi tare da haɗin gwiwar Cibiyar Kimiyyar Ma'adanai. Gabaɗaya, an zaɓi mutane 100 daga mazaɓar don cin gajiyar wannan shirin. An horar da mahalartan akan dubarun haƙar ma'adinan a zahiri sannan kuma aka horar da su kan amfani da kayan aikin zamani da na'urori wajen sarrafa ma'adanai a ɗakunan gwaje-gwaje na Cibiyar. An gudanar da shirin horon na tsawon mako guda.

A ƙarshen shirin horon, kowane mahalarci ya samu Naira Dubu Goma (N100,000), takalman shiga daji, safar hannu, takunkumin rufe fuska, hula mairufe kai, rigar ruwan sama, takardar shaidar horo, da lasisin haƙar ma'adinai.


















# Samar da fitulun hasken rana a mazaɓar Anka/Mafara

**Kuɗin Aiki: N30m** **Matsayin Aiki: An Aiwatar**

Daga tattaunawar da muka yi da babban mai taimaka wa ɗan majalisar, mun fahimci cewa an sawo fitulun titi masu amfani da hasken rana guda 70 aka sa su a waɗannan wurare: Titin Tsakuwa, Titin Yarkofa, Titin Masallacin Juma'a na Biyu, Titin Yan Hudu, Titin Kwaren Damma, da GGC Mafara.











05



Hon. Umar Dangaladima

Mazaɓar

Kaura/Birnin Magaji

# Yawan Ayyukan da aka Gabatar

# 4

# Sakamako

2

An Aiwatar

2

Ba a yi ba

## Samar da mota ƙirar Toyota Hilux a Mazaɓar Kaura/Birnin Magaji

Kuɗin Aiki: N22m Yanayin Aiki: An Aiwatar

Za mu iya tabbatar da cewa an sayi mota ƙirar Toyota Hilux a mazabar. Sai dai abin da muka gane shi ne, motar har yanzu tana hannun ɗan majalisar ba domin moriyar jama'a ba. Da muka ci gaba da bincike, mun gano cewa ana amfani da motar ne wajen daukar jami'an tsaro yayin zuwa ziyarar ta'aziyyar na ɗan majalisar da kuma sauran ayyukansa na ƙashin kai. Wannan aikin a zahiri ba shi da wani tasiri ga muradun al'ummomin mazaɓar gaba ɗaya.

## Tallafin a kan yin fina-finai ga matasa da mata a Kaura/Birnin Magaji

Kuɗin Aiki: N75m Matsayin Aiki: Ba a yi ba

Za mu iya tabbatar da cewa ba a aiwatar da wannan aikin ba. Ƙungiyarmu ba ta iya kafa wata shaida ta aiwatar da shi ba kuma al'ummar ba su san da shi ba.

## Samar da mota ƙirar Toyota bos mai ɗaukar mutane 18 a Mazaɓar Kaura/ Birnin Magaji

Kuɗin Aiki: N24m Matsayin Aiki:An Aiwatar

Za mu iya tabbatar da cewa an sayi mota ƙirar Toyota mai ɗaukar mutune 18 a mazaɓar. Sai dai kuma motar tana hannun ɗan majalisar ba domin yin amfani ko wata bukata ta al'umma ba. Mun gano cewa ana amfani da motar ne wajen harkokin siyasa; kamar ɗaukar jami'an jam'iyya zuwa harkokin siyasa, ziyarce-ziyarce, yin ta'aziyya, da kuma amfani da motar wajen wasu ayyuka na ƙashin kai na ɗan majalisar. A haƙiƙani wannan aikin ba shi da wani tasiri ga muradun al'ummar mazabar.

## Tallafin a kan yin fina-finai ga matasa da mata a Kaura/Birnin Magaji

Kuɗin Aiki: N50m Matsayin Aiki: Ba a yi ba

Za mu iya tabbatar da cewa ba a aiwatar da wannan aikin ba. Ƙungiyarmu ba ta iya kafa wata shaida ta aiwatar da shi ba kuma al'ummar ba su san da shi ba.

06

# Yawan Ayyukan da aka Gabatar

10

Sakamako



**Sen. Sahabi Ya'u**

Mazaɓar

Zamfara ta Arewa

09 An Aiwatar

1 Ba a ayi ba

# Horarwa ga mata da matasa akan sana'o'i daban-daban a Mazaɓar Zamfara ta Arewa

**Kuɗin Aiki: N50m**

**Matsayin Aiki: An Aiwatar**

An gabatar da wannan shirin horaswa ga mutane kusan 150 da aka zaɓo daga dukkan ƙananan hukumomin da ke mazaɓar ɗan majalisar dattijawan. An gudanar da bikin ƙaddamar da shirin ne a ɗakin taro na Kwalejin Kimiyya da Fasaha ta Tarayya ta Kaura Namoda, inda daga bisani aka gabatar da darussan horaswa ga mahalarta taron.

An horar da mahalarta taron akan sanin ilimin na'ura mai kwakwalwa da kuma kasuwanci. An gudanar da horon na tsawon makonni uku (3). Bayan darussan horon an baiwa kowane mahalarci Kwamfuta ko keken ɗinki .










# Bayar da kayan abinci ga 'yan gudun hijira a wurare daban-daban a Mazaɓar Zamfara ta Arewa

**kuɗin Aiki: N40m** **Matsayin Aiki: An Aiwatar**

A bisa tsarin aiwatar da wannan aikin, an kai agajin kayayyaki zuwa ga sansanonin 'yan gudun hijira a Shinkafi, Kaura Namoda da Zurmi. Kayan agajin da aka bayar sun haɗa da kayan abinci da sauran abubuwan bukatun yau da kullum. An kuma bayyana cewa an raba kusan buhunan shinkafa da gero 100 da katifu 100 da barguna 100 a kowane sansanonin ‘yan gudun hijira da aka halarta.



















# Bayar da kayan kulawa da lafiya ga 'yan gudun hijira a wurare daban-daban cikin Mazaɓar Zamfara ta Arewa


**kuɗin Aiki: N40m** **Matsayin Aiki: An Aiwatar**

Sansanonin 'yan gudun hijirar da suka amfana daga rabon kayan abinci da sauran abubuwan bukatu a baya su kuma ne sukaci gajiyar wannan shirin. A ƙarƙashin wannan shirin, an raba kujeru, kayan aikin asibiti kamar gadaje, shimfiɗu, tebura da magunguna a kowane sansanonin 'yan gudun hijirar da aka ziyarta. Bugu da kari, an samar da kayan girki kamar tukwane da sauran kayan masarufi da kuma babura da injunan samar da wutar lantarki.











# Samarda fitulun titi masu aiki da hasken rana a garin Zurmi a Karamar Hukumar Zurmi da Kungurki a Karamar Hukumar Kaura Namoda cikin Mazaɓar Zamfara ta Arewa.

Kuɗin Aiki: N100m

Matsayin Aiki: An Aiwatar

A ƙarƙashin wannan aikin, mun sami labarin cewa an sayo fitilun titi masu amfani da hasken rana kuma an sanya su a wasu takamaiman wurare a Zurmi, da Kaura Namoda. Kodayake, ba mu iya tabbatar da ainihin adadin fitilun titi da aka sanya ba.









# Koyar da Sana'o'i daban-daban da Samar da Tallafi ga Mata da Matasa a Zamfara ta Arewa

Kuɗin Aiki: N100m

Matsayin Aiki: An Aiwatar

Kimanin mutane 350 ne suka ci gajiyar wannan aikin a cikin wannan mazaɓar ɗan majalisar dattijai. An horar da waɗanda suka ci gajiyar akan dabarun kiwon dabbobi (kiwon kaji da akuya), dabarun haɗa na'urorin kama tashoshin talbijin mai aiki da tauraron dan adam, da ɗinkin keke, da kuma ɗinkin hannu. An gudanar da shirin horon na tsawon makonni uku (3) kuma kowane wanda aka horar ya samu alawus na Naira dubu biyar ne (N5,000) a kowane mako.


















# Kammala aikin ruwan Kaura-Namoda a Mazaɓar Zamfara ta Arewa.

**Kuɗin Aiki: N150m** **Matsayin Aiki: An Aiwatar**

Wannan aikin da aka aiwatar yana da alaƙa da Ayyukan Samar da Ruwa na mazaɓar ɗan majalisar dattijai na Zamfara ta Arewa wanda aka tsara a cikin Ayyukan Raya Kasa na Mazaɓun Tarayya na shekarar 2019. Musamman wannan aikin ya tanadi sayen bututu sama da 800 da tankunan sama da za a haɗa da Dam ɗin. Don haka aikin ya haɗa da gina ramukan karkashin kasa na bututun da za a haɗa shiyar Sabon Gari, da shiyar Low Cost da shiyar Gidan Nepa da madatsar ruwa (Dam).





# Gina rijiyoyin burtsatse na tuƙa-tuƙa a mazaɓar Zamfara ta Arewa.

**Kuɗin Aiki: N20m** **Matsayin Aiki: An Aiwatar**

Majiyar mu wajen bin sawun aiki ta nuna cewa za a haƙa rijiyoyin burtsatse tuƙa-tuƙa ne guda 22 a wannan mazaɓar ɗan majalisar dattijai. Sai dai ba za mu iya tabbatar da cewa an haƙa dukkan rijiyoyin burtsatsen a mazaɓar ba, amma daga wuraren da muka ziyarta mun ga wasu rijiyoyin burtsatse da aka haƙo, wanda da alama an aiwatar da mafi yawan aikin.





# Gina Gada a kan Kogin Sakajiki a Mazaɓar Zamfara ta Arewa.

Kuɗin Aiki: N200m

**Matsayin Aiki: An Aiwatar**

Tabbas wannan aikin da aka aiwatar yana da matuƙar muhimmanci ga al'ummar yankin bisa la'akari da matsalolin zirga-zirgar da suke fuskanta a lokutan damina. An kuma gina gadar cikin watanni shida kamar yadda aka tanada a jadawalin aikinta. Kyakkyawan aikin da aka yi yana da ban sha'awa a fili, kuma babu shakka cewa kwalliya ta biya kuɗin sabulu akan wannan aikin.







# Aikin Gina Hanyar Kaura-Yankaba a cikin Mazaɓar Zamfara ta Arewa

Kuɗin Aiki: N200m

**Matsayin Aiki: An Aiwatar**

Shi ma wannan aikin da aka aiwatar yana da matuƙar muhimmanci ga al'ummar yankin bisa la'akari da matsalolin zirga-zirgar da suke fuskanta a lokutan damina. Hanyar da ta hada Yankaba da Kaura an gina ta cikin watanni shida kamar yadda aka tanada a jadawalin aikin. Kyakkyawan aikin da aka yi yana da ban sha'awa a fili, kuma babu shakka cewa kwalliya ta biya kuɗin sabulu akan wannan aikin.







# Bada Tallafi a cikin Mazaɓar Zamfara ta Arewa

kuɗin Aiki: N14.285m Matsayin Aiki: Ba a yi ba

Za mu iya tabbatar da cewa ba a aiwatar da wannan aikin ba. Ma'aikatanmu ba su sami wata shaida akan aiwatar da shirin ba daga al'ummar mazaɓar.

07

Yawan Ayyukan da aka

# Gabatar

3

## Sakamako

3

An Aiwatar

0

Saura



**Hon. Ahmed Muhammad Bakura**

Mazaɓar

## Bakura/Maradun

# Horo da Tallafawa Matasa da Mata a ciki Mazaɓar Bakura/Maradun

**Kuɗin Aiki: N60m** **Matsayin Aiki: An Aiwatar**

An zaɓo matasa 1000, waɗanda suka ƙunshi duka jinsi biyu, don wannan shirin na bada horo. An horar da matasan dabarun noman shinkafa. Mahalarta wannan shirin kuma sun samu laccoci kan munin kalaman nuna ƙiyayya. An gudanar da shirin horon na tsawon mako guda, kuma a karshen horon kowanne daga cikin mazan ya samu tallafin Naira dubu ashiri (N20,000), yayin da mata suka samu Naira dubu goma (N10,000) kowacce.


















# Horarwa akan ayyukan haƙar ma'adinai ga masu aikin hannu a mazaɓar Bakura/Maradun

**Kuɗin Aiki: N31m** **Matsayin Aiki: An Aiwatar**

An aiwatar da wannan shirin a wajen Jiha. Shirin horon ya gudana ne a Jos, kuma an aiwatar da shi tare da haɗin gwiwar Cibiyar Kimiyyar Ma'adanai. Gabaɗaya, an zaɓi mutane 100 daga mazaɓar don cin gajiyar wannan shirin. An horar da mahalartan akan dubarun haƙar ma'adinan a zahiri sannan kuma aka horar da su kan amfani da kayan aikin zamani da na'urori wajen sarrafa ma'adanai a ɗakunan gwaje-gwaje na Cibiyar. An gudanar da shirin horon na tsawon mako guda.

A ƙarshen shirin horon, kowane mahalarci ya samu Naira Dubu Goma (N100,000), takalman shiga daji, safar hannu, takunkumin rufe fuska, hula mairufe kai, rigar ruwan sama, takardar shaidar horo, da lasisin haƙar ma'adinai.









# Samar da famfunan ruwa na rijiyoyin burtsatse a mazaɓar Bakura/Maradun

**Kuɗin Aiki: N30m** **Matsayin Aiki: An Aiwatar**

Wannan aikin ya ƙunshi gina rijiyoyin burtsatse guda 20 a ƙananan hukumomin biyu dake mazaɓar. Mun sami damar ganin wasu ciki har da allunan alamar a wasu wuraren da aka zaɓa a cikin mazabar amma ba mu iya tantance duk sauran wuraren ba. Duk da haka, tuntuɓar mutane daban-daban da muka yi daga baya ta wayar sadarwa sun nuna cewa da alamar an yi aikin da dama.

Wuraren da aka samar da famfunan tuƙa-tuƙa sun hada da mazaɓar Bakura, mazaɓar Dan Manau, Yarkofoji, Yargeda a cikin Tungar Kalgo, Damri, Rini, Shiyar Galadima, Nasarawa, Dakko, Ɗan Kadu duk a Karamar Hukumar Bakura. A Karamar Hukumar Maradun, wuraren sun haɗa da Maradun ta Kudu, Maradun ta Arewa a Shandame, Tsibiri, Damaga a cikin Gamagiwa, Gora, Jan Bako, Dan Baza, Dosara, Birnin Kaya da Kaya.










# 08



**Hon. Bello Hassan Shinkafi**

Mazaɓar

## Shinkafi/Zurmi

Yawan Ayyukan da aka

## Gabatar

# 5

## Sakamako

| 4 | 1 |
|---|---|
| An Aiwatar | Ana kan yi |

# Horo da tallafawa matasa da mata a mazaɓar Shinkafi/Zurmi

**Kuɗin Aiki: N35m** **Matsayin Aiki: An Aiwatar**

An gudanar da wannan shirin horon ne a zauren sakatariyar gwamnatin Karamar Hukumar Shinkafi. Jimlar adadin membobin matasa 100 ne suka amfana daga wannan shirin. An horar da su kan ayyukan dinki, noma, yin sabulu da yin man shafawa. Kodayake bamu san takamaiman ƙa'idojin zaɓen waɗanda aka horas ba.











# Katange babbar asibitin Shinkafi

**Kuɗin Aiki: N21m** **Matsayin Aiki: An Aiwatar**

Babban asibitin da ke Shinkafi ta shafe shekaru a cikin rashin cikakkar kariyar muhallinta saboda rashin shingewa, kuma hakan yana haifar da matsalar tsaro. A lokacin ziyararmu ta farko, an fara aiki da gina babbar kofar shiga da shingen gaban, amma akwai sauran ayyuka da yawa da za a yi saboda girman wurin. Sai dai, a ziyarar da muka kai ta karshe, an kammala aikin; anyi fenti kuma an gina katangar da ginshiƙai don ƙara ingancin aikin.







# Gina ajujuwa uku da kujeru a Kadawa da Boko cikin Karamar Hukumar Zurmi, a mazaɓar Shinkafi/Zurmi

**Kuɗin Aiki: N30m** **Matsayin Aiki: An Aiwatar**

An aiwatar da wannan aikin yadda ya kamata. Lokacin da ma'aikatanmu suka ziyarci wurin da ake aikin, sun gudanar da cikakken nazari domin tabbatar da ingancin aikin da aka yi kuma suka gamsu sosai. An gina ajujuwa uku (3) tare da kujeru da teburan ɗalibai. Wannan aikin ba shakka zai ƙara ma matsayin ilimi na yankin kima tare da inganta matsayin ilmi saboda ƙarancin tallafin da ilimi keda a yankin.





# Gina Cibiyar kula da ƙananan yara a Shinkafi a mazabar Shinkafi/Zurmi

**Kuɗin Aiki: N50m** **Matsayin Aiki: An Aiwatar**

An aiwatar da wannan aikin yadda ya kamata. Lokacin da ma'aikatanmu suka ziyarci wurin da ake aikin, sun gudanar da cikakken nazari domin tabbatar da ingancin aikin da aka yi kuma suka gamsu sosai. An samar da gina da ta ƙunshi azuzuwa, banɗakuna, da filin wasan yara na zamani, kuma an sanya kayan aiki da sauran abubuwan da ake bukata wajen koyar da yara ƙanana. Wannan aikin ba shakka zai ƙara kima ga matsayin ilimi a yankin.





# Gina ɗakunan karɓar haihuwa biyu tare da kayan aiki a Lamba da Kware a mazabar Shinkafi/Zurmi

**Kuɗin Aiki: N35m**

**Matsayin Aiki: An Aiwatar**

Ana cikin aiwatar da wannan aikin gaba ɗaya lokacin da ma'aikatanmu suka ziyarci wurin aikin. Tawagar ta gudanar da bincike domin kimanta ingancin aikin da aka yi kuma suka ga aikin yana da ban sha'awa. Bugu da kari, tawagar ta kuma gano cewa an sayo dukkan kayayyakin da ake bukata kuma suna ajiye a wurin aikin. Wannan aikin ba shakka zai ƙara kima ga ayyukan kula da lafiya a yankin.









# 09

Yawan Ayyukan da aka

# Gabatar

# 3

# Sakamako



**Hon. Shehu Ahmad**

Mazaɓar

## Maru/Bungudu

3

An Aiwatar

0

Saura

# Kayayyakin tallafi da horar da matasa da mata a mazabar Maru/ Bungudu

**Kuɗin Aiki: N41m** **Matsayin Aiki: An Aiwatar**

An gudanar da wannan aikin kashi-kashi ne, amma a jimilla an zaɓi mahalarta kusan 600 daga gundumomi 14 na mazaɓar. An horar da waɗanda suka ci gajiyar aikin fasahar kwamfuta kuma a ƙarshe kowane ya sami tallafin sabuwar Kwamfuta. Bamu iya tantance ƙa'idojin da aka bi ba wajen zaɓen waɗanda sukaci gajiyar wannan shirin ba.







# Samar da kayayyakin injunan niƙa da keken ɗinki domin tallafawa Matasa Maza da Mata

**Kuɗin Aiki: N50m** **Matsayin Aiki: An Aiwatar**

An zaɓi adadin mutune 300 don cin gajiyar wannan aikin. An horar da waɗanda suka ci gajiyar shirin kan dogaro da kai, kuma a karshen shirin kowane ɗaya daga cikin mahalarta taron ya samu kyautar keken dinki yayin da mahalartan mata aka baiwa kowacce injin niƙa. An rarraba jimlar injunan niƙa 150 da keken ɗinki 150







# Rage ƙalubalen rikice-rikice da samun zaman lafiya mai ɗorewa domin maganin tashe-tashen hankula da samar da tsaro a mazaɓar Maru/Bungudu

**Kuɗin Aiki: N30m** **Matsayin Aiki: An Aiwatar**

An ƙirƙiro wannan aiki ne domin magance matsalar rashin tsaro da ya addabi mazaɓar a shekarun baya. An zaɓo wadanda suka amfana daga gundumomi 21 na mazaɓar. Babban bikin buɗe shirin ya samu halartar Gwamnan wanda mataimakinsa ya wakilta. Dukkan masu rike da muƙaman gargajiya na mazabar ma sun halarci bikin. Shirin na kwanaki uku ya ƙunshi jerin laccoci da ƙwararru suka gabatar kan magance rikice-rikice, warware rikici da sasantawa. Domin ba wa shirin fasaha cikin nishaɗI, an ware zango na musamman akan waƙoƙi kan illolin rashin tsaro a jihar.

A karshen shirin an bai wa kowanne daga cikin mahalarta kyautar kuɗi ko kaya.









10

Yawan Ayyukan da a ka

# Gabatar

4

# Sakamako



Sen. Lawali Hassan

Mazaɓar

Zamfara ta Yamma

0

An Aiwatar

4

Ba a yi ba

# Tallafi ga matasa da mata a mazaɓar Zamfara ta Yamma.

**Kuɗin Aiki: N120m** **Matsayin Aiki: Ba a yi ba**

Za mu iya tabbatar da cewa ba a aiwatar da wannan aikin ba. Ma'aikatanmu ba su samu wata shaida ta aiwatar da shi ba kuma al'ummar mazaɓar ba su san da aikin ba.

# Samar da tallafin injunan casar shinkafa a mazaɓar Zamfara ta Yamma

**Kuɗin Aiki: N50m** **Matsayin Aiki: Ba a yi ba**

Za mu iya tabbatar da cewa ba a aiwatar da wannan aikin ba. Ma'aikatanmu ba su samu wata shaida ta aiwatar da shi ba kuma al'ummar mazaɓar ba su san da aikin ba.

# Tallafawa matasa da mata a Mafara, Bakura da Maradun, Zamfara ta Yamma

**kuɗin Aiki: N50m** **Matsayin Aiki: Ba a yi ba**

Za mu iya tabbatar da cewa ba a aiwatar da wannan aikin ba. Ma'aikatanmu ba su samu wata shaida ta aiwatar da shi ba kuma al'ummar mazaɓar ba su san da aikin ba.

# Tallafawa matasa da mata a Anka, Gummi da Bukkuyum a Zamfara ta Yamma

**Kuɗin Aiki: N44.285m** **Matsayin Aiki: Ba a yi ba**

Za mu iya tabbatar da cewa ba a aiwatar da wannan aikin ba. Ma'aikatanmu ba su samu wata shaida ta aiwatar da shi ba kuma al'ummar mazaɓar ba su san da aikin ba.

# TSARIN AUNA ƘWAZON ƊAN MAJALISA


Tsawon shekaru al’ummar jihar Zamfara ba su da masaniyar ko wace irin kimar wakilcin majalisun tarayya ke da shi wajen inganta rayuwarsu da mulkin dimokuradiyya. Wannan duk ya faru ne saboda rashin sanin ayyukan ɗan majalisar tarayya da kuma kuskuren da suke yi na ɗora wasu bukatu a kan wakilansu wanda ke haifar da rashin bin ƙa'iodijin tafarkin gaskiya. A yanzu muna ƙoƙarin ilimantar da al'umma a kan wannan batu ta hanyar ingantattun dabarun faɗakarwa. Don haka mun buɗe ayyukan mazaɓu ga jama’a. Manufarmu ita ce mu ƙaddamar da sa ido ta hanyoyin bin diddiƙin ayyuka daga wajen al'umma ta yadda za su rungumi haƙƙin kayansu tare da iya jan-akalar wakilansu. Dangane da haka, mun ƙirƙiro da wani tsarin auna ƙwazon 'yan majalisa a bisa abubuwa uku da ke da dangantaka da za ta sauƙaƙa yaƙi da cin-hanci da rashawa da inganta al'amuran zamantakewa a cikin Jiha.

# Tsarin Bada Lambar Girma

Fihirisar A na kimanta ko 'yan ƙasa sun tsunduma cikin zaɓe da tsarin aiwatarwa. Duk wani nau'i na haɗin gwiwar jama'a da aka yi amfani da shi zai sami maki 1 rashinsa maki 0.

Fihirisar B na kimanta matakin aiwatar da duk ayyukan da ƴan majalisa suka gabatar.

Fihirisar C na kimanta yanayin ayyukan da aka gabatar tsakanin manyan ayyuka da ayyukan bada tallafi/horaswa.




**Yawan Ayyukan da aka aiwatar**

**Manyan Ayyuka da aka Gabatar**

# Kwazon Dan Majalisa a kan Fihirisar A

Fihirisar A tana kimanta ko anyi amfani da wasu dabarun tuntuɓar al'umma, kamar tarurrukan gari, wajen tsarin zaɓe da aiwatar da ayyukan raya ƙasa na mazaɓun tarayya.

| Dan Majalisa | Sakamako |
|---|---|
| SEN. MUHAMMAD HASSAN | 0 |
| SEN. SAHABI YA'U | 0 |
| SEN LAWALI HASSAN | 0 |
| KABIRU AMADU | 0.4 |
| SHEHU AHMED | 0 |
| KABIRU YAHAYA | 0 |
| AHMAD MUHAMMAD | 0 |
| SULAIMAN MUHAMMAD GUMMI | 0 |
| UMAR DAN GALADIMA | 0 |
| BELLO HASSAN SHINKAFI | 0 |

# Kwazon Ɗan Majalisa a kan Fihirisar B

Wakilan da ke da matsayi mafi girma a kan Fihirisar B sun tabbatar da cikakken aiwatar da ayyukan da suka gabatar. Kowane aikin da aka kammala yana ɗaukar maki 1 yayin da ayyukan da ke gudana yana ɗaukar 0.5. Waɗanda ke da karancin matsayi ba su tabbatar da aiwatar da ayyukan da suka gabatar ba.

| Ɗan Majalisa | Sakamako |
|---|---|
| SULAIMAN MUHAMMAD GUMMI | 0.35 |
| KABIRU AMADU | 0.35 |
| SHEHU AHMED | 0.35 |
| KABIRU YAHAYA | 0.35 |
| AHMAD MUHAMMAD | 0.35 |
| SEN. SAHABI YA'U | 0.32 |
| BELLO HASSAN SHINKAFI | 0.32 |
| SEN. MUHAMMAD HASSAN | 0.30 |
| UMAR DAN GALADIMA | 0.26 |
| SEN LAWALI HASSAN | 0 |

# Kwazon Ɗan Majalisa a kan Fihirisar C

Wakilan da ke da matsayi mafi girma akan Fihirisar C sun ba da fifikon wajen gabatar da manyan ayyuka a mazaɓarsu. Waɗanda ke da ƙaramin matsayi kuwa sun gabatar da ayyukan da ba su da kima ga manyan buƙatun al'ummar mazaɓun.

| Ɗan Majalisa | Sakamako |
|---|---|
| BELLO HASSAN SHINKAFI | 0.20 |
| SULAIMAN MUHAMMAD GUMMI | 0.17 |
| SEN. SEN. SAHABI YA'U | 0.14 |
| SEN. M UHAMMAD HASSAN | 0.13 |
| KABIRU YAHAYA | 0.08 |
| AHMAD MUHAMMAD | 0.08 |
| SEN LAWALI HASSAN | 0 |
| KABIRU AMADU | 0 |
| SHEHU AHMED | 0 |
| UMAR DAN GALADIMA | 0 |

# Matsayin Karshe na'Yan Majalisa

| Matsayi | Dan Majalisa | Sakamako |
|---|---|---|
| 1 | HON. KABIRU AMADU | 0.75 |
| 2 | HON. BELLO HASSAN SHINKAFI | 0.52 |
| 2 | HON. SULAIMAN MUHAMMAD GUMMI | 0.52 |
| 4 | SEN. SAHABI YAÚ | 0.46 |
| 5 | SEN. MUHAMMAD HASSAN | 0.43 |
| 5 | HON. KABIRU YAHAYA | 0.43 |
| 5 | HON. AHMAD MUHAMMAD | 0.43 |
| 8 | HON. SHEHU AHMED | 0.35 |
| 9 | HON. UMAR DAN GALADIMA | 0.26 |
| 10 | SEN. LAWALI HASSAN | 0 |

# Manyan ƙalubalen da aka fuskanta wajen bin diddiƙin ayyukan mazaɓu na shekarar 2020 a Jihar Zamfara

## Rashin Yanayin Tsaro

Jihar Zamfara dai na daga cikin wuraren da aikin ta'addanci yayi ƙamari a yankin Arewa maso Yamma wanda hakan ya haifar da bala'o'i. Wannan ƙalubale ya hana ma'aikatanmu bin wasu ayyuka a yankunan da abin ya fi shafa. Muna fatar lamarin tsaro zai inganta.

## Yawan Ayyukan Tallafi

Kalubalen da ke tattare da tanadin ayyukan bada tallafi suna da yawa. Babban matsalar da ma'aikantanmu suka fuskanta wajen bin diddiƙin ire-iren waɗannan ayyukan a wannan shekara ita ce rashin iya tantancen kimar su. Alfanun waɗannan ayyukan taƙaitacce ne kuma waɗanda su ke cin gajiyar ayyukan 'yan koren siyasar wakilan ne ba mutanen da suka fi buƙatun neman tallafi ba ne.

## Rashin Sunayen Wuraren Gudanar da Ayyuka

Don ingantaccen aikin bin diddiƙin, ana buƙatar takamaiman sunayen wuraren aikin a lokacin gabatarwa. Abin baƙin ciki shine, babu irin wannan bayani kuma saboda da haka al'ummomi da ƙungiyoyin jama'a ba su san wuraren ba wanda hakan na hana su damar sa ido da tabbatar da aiwatar da ayyukan kamar yadda ya kamata. Babban misalin irin wannan matsala shine na samar da rijiyoyin burtsatse a mazaɓun Zamfara ta Arewa da Bakura/Maradun.

## Rashin Tsarin Tuntuɓar Al'ummar Mazaɓu

Ɗaya daga cikin ƙalubalen da ke gurgunta tasirin waɗannan ayyuka shine na rashin cikakkun bayanai game da su da na wayar da kan jama'a da shiga cikin tantancewa da aiwatar da ayyukan. Don haka, yawancin ayyukan da aka gabatar ba su magance takamaiman ƙalubalen da mazaɓun ke fuskanta.

| N1.247bn | N1.142bn |
|---|---|
| Ayyukan ba da Tallafi | Manyan Ayyuka |

ZamTracka

Data | Civic Advocacy | Social Accountability

Follow up and track implementation of public projects within your vicinity

Upload pictures, add comments, send feedback to institutions

Announce and share with your friends, family and thousand across the state

Continue to engage.

No. 40, Sadiqu Sadiq Road,
Tudun Wada, Gusau, Zamfara State.

f/t @ZamTracka

ZamTracka@gmail.com

# #AskQuestions